**EPISODE 12**

**CHARACTERS**

*Laraba*

*Alhaji Bature*

*Husseini*

*Asabe*

*Hannah*

*Tanko*

**EPISODE 12, SCENE 1**

**Northern Kaduna. Alhaji Bature's Store Near The Motor Park. Morning**

1. **MUSIC:** **THEME MUSIC**
2. **SFX:** **HEAVY VEHICULAR TRAFFIC. A MIX OF HAUSA, INDIAN AND EVEN IGBO HIGHLIFE MUSIC BLARING FROM DIFFERENT CORNERS OF THE MOTOR PARK. CONDUCTORS CALLING PASSENGERS TO DIFFERENT PARTS OF THE METROPOLIS.**
3. **LARABA:** Ina yini Mallam... Ina son in saya wasu kayayyaki. An gaya mun cewa zan samu farashi masu kyau a nan.
4. **ALHAJI B:** Ina yini Mallama. Haka ne, a nan ne zaki samu ingantattun kayayyaki a farashi masu sau*k*i sosai. Sunana Alhaji Bature! Muna da duk abun da kike bu*k*ata a farashi masu kyau.

5. **LARABA:** **(LAUGHING)** Na gode Mallam. Ina ta jin labarin ka da ta shagon nan.

6. **ALHAJI B:** Ina fatan kin ji labari mai kyau ne. Daga rigarki na san ke nas ce. Haka ne ko?

7. **LARABA:** Haka ne Alhaji. Ni Nas ce......

8. **ALHAJI B:** **(CUTTING IN EXCITEDLY)** Ki dakata na canka. Kece Nas Laraba, sabuwar nas na *k*aramar asibitinmu ko!

9. **LARABA:** **(LAUGHING SHYLY)** Eh Alhaji! Nayi mamaki ka san sunana.

10. **ALHAJI B:** **(WITH EXCITEMENT)** Yaya bazan sani ba? Ina ta jin labarai masu kyau a game dake. Nas Laraba, sannunki da zuwa shago na.

11. **LARABA:** Ina maka godiya sosai da wannan maraba. Mai Unguwa ya gaya mun abubuwa masu kyau a game da kai. Ana girmama ka a wannan garin, kuma ina murnar ganewa da kai.

12. **ALHAJI B:** Ina murna da cewa kin ji abubuwa masu kyau a game da ni. Kin san ina *d*aukar matsayina na mai gina al'umman nan da muhimmanci.

13. **LARABA:** Yana da kyau Mallam. Daman Mai Unguwa ya ce zai tambaye ka ko zaka shiga Kwamitin Kiwon Lafiya ta Al'umma da aka kafa, amma ina ganin kayi tafiya lokacin da muka yi taronmu ta farko.

14. **ALHAJI B:** **(SLIGHTLY BOASTING)** Eh, haka ne, nayi tafiya lokacin. Dubai da Legas, domin *d*an kasuwanci na.

15. **LARABA:** Sannu da aiki Mallam. Yanzu da ka dawo, na san Mai Unguwa zai yi maka magana akan Kwamitin Kiwon Lafiya ta Al'umman da aka kafa.

16. **ALHAJI B:** Babu wata matsala. Amma kafin can, ki gaya mun wani abu akan sa mana Nas Laraba?

17. **LARABA:** Toh Alhaji Bature, an kafa kwamitin ne domin a nemi hanyoyin inganta lafiyar jikin al'umman garin nan ne.

18. **ALHAJI:** Haka yana da kyau Nas Laraba. Kuma ina gani kaman ke ce jami'ar wannan al'umma. Ina jin da*d*i na ga matasa kaman ki na tunanin inganta al'umma, ba wai su ringa tunanin abun da zasu iya kar*b*a daga al'umma ba.

19. **LARABA:** **(SHYLY)** Sai da yardar Ubangiji Allah! Na gode sosai Alhaji.

20. **ALHAJI B:** Na'am Nas Laraba. Ina nan ina jira na fara aiki a kwamitin nan naki.

21. **LARABA:** Na gode Alhaji. Ga kayan da nake so. Nawa ne duka?

22. **ALHAJI:** Ah Nas Laraba, kar ki damu da biya. Na ji labarinki, da kuma duk kyawawan ayyukan da kike yi a wannan garin. Wa ya san ko ni, ko kuma iyali na zasu nemi taimakonki wata rana. Don Allah ki *d*auka kayan kawai, babu damuwa!

23. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC.</u>**

**EPISODE 12, SCENE 2**

**NORTHERN KADUNA. HAJIA INNA'S HOME. LATE EVENING.**

24. **SFX:** **<u>NIGHT TIME QUIET. CRICKETS CHIRPING.</u>**

25. **HUSSEINI:** **(OFF MIC, CALLING OUT) (FRIENDLY)** Nas Laraba, yayi haka, idan kina da wata matsala kuma da makunnin wutan ki gaya mun ko kuma Hassan. **(PAUSES, THEN LAUGHS)** Toh sai da safe.

26. **SFX:** **<u>STEPS ON THE FOOT MAT. DOOR OPENS.</u>**

27. **HUSSEINI:** Darling Asabe. Yaya labari? **(PAUSES)** Haba, me ke damun ki? Fuskarki bai yi haske ba, kuma baki yi mun irin marabar da kika saba yi ba?

28. **ASABE:** Ban jin da*d*i da kai, shi yasa Husseini.

29. **HUSSEINI:** **(SURPRISED)** Baki jin da*d*i da ni? Me nayi?

30. **ASABE:** Ban son yadda kake gaisawa da matan can, Laraba. Kana ta fara'a kana ta*d*i da ita.

31. **HUSSEINI:** Menene laifin yin hul*d*a da matan da take zama a gida *d*aya da ni?

32. **ASABE:** Komai ne laifi Husseini. Komai. Gaskiyar magana shine bana son kana magana tare da ita.

33. **HUSSEINI:** **(SHOCKED)** Yanzu zaki gaya mun wa ya kamata na yi magana da Asabe?

34. **ASABE:** Bazan iya gaya maka wa zaka yi magana da ba. Ni dai na san cewa bana son kana magana da matan nan Laraba.

35. **HUSSEINI:** Me yasa baki son ta? Tana kama da mace mai kirki da kamun kai.

36. **ASABE:** **(VOICE RISING)** Baka jin abun da mutane ke fa*d*i game da Nas Laraba da kai da Hassan ba?

37. **HUSSEINI:** **(SHOCKED)** Har da Hassan a cikin wannan maganan? Me suke cewa?

38. **ASABE:** Mutane na kokwanton wane a cikinku zai aure Laraba.

39. **HUSSEINI:** **(AMUSED)** Ashe akwai mutane marasa aiki a garin nan da ke ya*d*a banzan maganganu da gulmace-gulmace? **(LAUGHS)**

40. **ASABE:** **(NOT AMUSED)** Husseini, ba abun dariya bane. Me ya baka dariya a wannan maganan?

41. **HUSSEINI:** **(CHUCKLING)** Asabe me yasa kike barin banzan gulma ta dame ki? **(PAUSES)** Ba ma ni *d*aya ba, mu biyu ake zargin zamu zama mijin Nas Laraba! **(LAUGHS HEARTILY)** Gaskiya da ban-dariya!

42. **ASABE:** Eh! Tanko ya ce wai ana ta maganan ne a layinmu. Ya ma ce wai mutane na sa ku*d*i a ga ko kai ne, ko kuma Hassan ne zai yi rinjaye ya samu Laraba.

43. **HUSSEINI:** (**BURSTS INTO LAUGHTER)** O-ho! Matata kenan, wato Tanko ne yake wannan gulman ko? Yaushe Tanko ya fara fa*d*in gaskiya a magana?

44. **ASABE:** Na san Tanko ya cika gulma amma ni dai bana son Laraba ta zauna a gidanmu. Kaga an riga an fara yin gulma Husseini.

45. **HUSSEINI:** Kin ga Asabe, kar ki dame wannan kyakkyawan kanki akan abun da baza ki iya canzaw ba. Hajiya Inna ce ta *d*auki Laraba kuma baza mu iya canzawa ba.

46. **ASABE:** Na sani, har na gaya wa Hajiya cewa bai dace Nas Laraba ta kama *d*aki a nan ba.

47. **HUSSEINI:** Kuma Hajiya ta saurare ki?

48. **ASABE:** A'a. Ta gaya mun wai ita tana son Laraba, kuma ta riga ta kar*b*i ku*d*in haya a hannunta, kuma babu wanda zai canza mata ra'ayi.

49. **HUSSEINI:** Kin ga abun da nake fa*d*a ko? Toh matata, ki kwantad da hankalinki. Babu *d*aya daga cikin ni ko Hassan da zai auri Laraba. Da ni da shi, matanmu duk sun ishe mu.

50. **ASABE:** Babu abun da zan iya yi, amma ni dai bana son Nas Laraba ta zauna tare da mu.

51. **HUSSEINI:** Ki kwantad da hankalinki masoyiyata. Komai zai tafi a daidai. Har kin sa na manta. Ga awarwaron da na kawo miki.

52. **ASABE:** (**EXCITED)** Oh maigida na, suna da kyau sosai. Kalli yadda duwatsun ke wal*k*iya. Na gode sosai maigida na.

53. **HUSSEINI:** Matata, kin san ban da idon kallon wata mata daban. Bani da wata dalili bayan yadda kika yi kyau da kika fara amfani da robar IUD.

54. **ASABE:** (**LAUGHING SHYLY)** Ai robar IUD na tazzara na ba wa jiki na lokaci ya huta domin na yi *k*wari da kyau wa kai da yaran.

55. **HUSSEINI:** Haka ne, kuma Asabe, zamu iya sake jiki da junanmu a kowanne lokaci ba tare da damuwan *d*aukan ciki ba shiri, har sai mun shirya.

56. **ASABE:** **(SHYLY)** Husseini, abun da kake tunani kenan yanzu?

57. **HUSSEINI:** **(TEASING)** Ta yaya bazan yi tunanin sa ba? Ina matu*k*ar murna da muke amfani da hanyan tazzara ta zamani. Kalli yadda kika zama; a cikin *k*oshin lafiya da kuma kyau kamar sabuwar amarya.

58. **ASABE:** **(LAUGHING FLIRTATIOUSLY)** Kai maigida, kallon da kake yi mini ke nana?

**EPISODE 12, SCENE 3**

**NORTHERN KADUNA. HAJIYA INNA'S HOUSE, LARABA'S ROOM**

59. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

60. **SFX:** **<u>KNOCK ON THE DOOR.</u>**

61. **LARABA:** **(OFF MIC)** Wanene? Shigo.

62. **SFX:** **<u>DOOR OPENS AND CLOSES</u>**

63. **LARABA:** **(SURPRISED)** Hannah! Allah Sarki! Sannu fa, ban san zaki zo ba.

64. **HANNAH:** **(LAUGHING)** Ban so ki san wai zan zo ne ai Laraba.

65. **LARABA:** **(EXCITED)** Hey! Ina farin cikin zuwanki. Yaya maigidanki?

66. **HANNAH:** Yana lafiya, ya ce na gaishe ki. Ga abun da na kawo miki.

67. **SFX:** **<u>RUFFLING OF SHOPPING BAGS.</u>**

68. **LARABA:** Har kin je kin yi mun sayayya. Na gode sosai. Kina tuna mun da Dr. Daoud wanda bai gushewa da kawo mun kyauta duk lokacin da yayi tafiya zuwa gida.

69. **HANNAH:** Wai! Wai!! Wanene Dr. Daoud me kawo miki kyaututtuka? Laraba! Ki bani labari!

70. **LARABA:** Dr Daoud likita ne a *k*aramin asibitin. Yana da kirki, kuma bai da*d*e da ya shaida mun yana son ya fara zance da ni.

71. **HANNAH:** **(EXCITED)** Wannan labari ne mai kyau! Ina miki murna! Sabuwar shiga kenan!

72. **LARABA:** Kar fa ki fara murna.

73. **HANNAH:** Meyasa?

74. **LARABA:** **(DRYLY)** Kar ki manta da sa'a ta. Ba da da*d*ewa bayan Dr. Daoud ya shaida mun nufinsa sai wata 'yar uwar aiki na Maria ta zo tana mun garga*d*i, wai shi nata ne.

75. **HANNAH:** **(COOLY)** Me kike tunani Laraba? Kina tunani wani na mallakan wani ne?

76. **LARABA:** Kin san meh Hannah, bana son fitina. Bana son na shiga hanyan wani, ina son kwanciyar hankali na ne kawai.

77. **HANNAH:** Ina ganin kina dai guduwa ne da cika ce wai baki son fitina. Bari nayi miki wata tambaya: kina ganin Dr. Daoud mutum ne da zai neme ki bayan yana soyayya da wata daban?

78. **LARABA:** Gaskiya, a’a. Kuma ma hujjar Nas Maria akan Dr. Daoud shine wai ita ta fara ha*d*uwa da shi.

79. **HANNAH:** Toh ina ganin sai ki tambaye Dr. Daoud kai tsaye ko yana da wata dangantaka da Nas Maria.

80. **LARABA:** Amma Hannah, wannan ba zai zama wani iri ba? Domin ban riga na bashi amsa cewa na amince da shi ba tukunna.

81. **HANNAH:** Ban tsammanin haka Laraba. Ko da baza ki amince masa bane ai sai kin bashi dalili. Sai ki tambaye shi, ki yanke shawara bisa da amsar da ya baki.

82. **LARABA:** Toh Hannah, zan tambaye shi in mun ha*d*u a asibitin.

83. **HANNAH:** Yayi kyau. Ta haka zaki san gaskiyar maganan.

84. **LARABA:** Amma ko da na gane cewa Dr. Daoud bai tare da wata, ina tsoron rashin sa’a dake biye da ni da mutanen da nake so. Bana son Dr. Daoud ya mutu kaman yadda Jallo da iyaye na da ‘yan-uwa na suka mutu.

85. **HANNAH:** Ki kwantad da hankalinki. Babu abun da zai faru da Dr. Daoud.

86. **LARABA:** Kin ga Hannah, baki gane bane. Munanan abubuwa sun cika faruwa da ni da mutanen da nake so.

87. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 12, SCENE 4**

**Northern Kaduna. Alhaji Bature’s Shop At The Motor Park. Late Afternoon.**

88. **SFX:** **<u>MOTOR PARK AMBIENCE.</u>**

89. **TANKO:** Barka dai Alhaji Bature, mai bada taimako ma matasa da masu nema a garin na!

90. **ALHAJI B:** **(AMUSED)** Barka dai Tanko. Yaya kake? Zaka yi tafiya ne? Me ya kawo ka tasha?

91. **TANKO:** A'a Alhaji Bature. Na zo ne na ga aboki na Husseini wanda ka taimaka wa har yana iya ciyar da iyalinsa.

92. **ALHAJI B.** **(LAUGHING)** Toh Tanko, taimakon mutane ha*kk*i ne a gare ni.

93. **SFX:** **<u>A THUD AS SOMETHING HEAVY FALLS.</u>**

94. **TANKO:** Yi ha*k*uri Alhaji. Ina fatan ban bata wani abu ba? Wa*d*annan fosta ne ko?

95. **SFX:** **<u>PAPERS RUSTLING.</u>**

96. **ALHAJI B:** Eh Tanko, mai buga takarda ne ya kawo mun fostan neman za*b*en yaron *d*an-uwa na, wanda ke takaran Kansalan *K*aramar Hukuma.

97. **TANKO:** Ranka ya da*d*e! Yaron dan-uwanka na da sa'a da ya samun babban jarumi mai na*d*in sarakai kamanka na bashi goyon baya.

98. **ALHAJI:** **(LAUGHING)** Amma kai Tanko da kake yawo a gari, ka san cewa ina jin da*d*in taimaka wa matasa da samari wajen samun wurare masu muhimmanci a al'umma.

99. **TANKO:** Yaya bazan san wannan ba? Duk gari na mamakin irin cin kasuwarka da kuma na*d*in sarakai da kake ta yi a garin nan.

100. **ALHAJI:** **(ENJOYING THE COMPLIMENTS)** Na gode Tanko. Ina fatan zaka taimaka ka ya*d*a wa*d*annan fostan. Zan tabbata an baka ladanka kaman yadda ya kamata.

101. **TANKO:** Sosai ma Alhaji. Alhaji, yi mun garfara, amma Husseini na sane da neman za*b*en da yaron *d*an-uwanka ke yi?

102. **ALHAJI:** (**SURPRISED)** Ban sani ba. *K*ila bai sani ba. Ya kamata na gaya wa Husseini burin yaron ne?

103. **TANKO:** (**GLEEFULLY)** Yi ha*k*uri Alhaji, amma *d*an-uwan Husseini na neman wannan matsayin da yaron *d*an-uwanka ke nema.

104. **ALHAJI:** (**SHOCKED)** Ta yaya Hassan zai nema takaran ba tare da ya gaya mun tukunna ba? Ni nake za*b*in 'yan takaran wannan matsayin daga wannan garin.

105. **TANKO:** Da naga fostan Hassan a gidan Hajiya Inna na *d*auka kai ne kake goyon bayansa, kamar yadda kake taimakon *d*an-uwansa Husseini a kasuwancin mai-shayinsa.

106. **ALHAJI:** **(UPSET)** Ban san meyasa Hassan bai ga ya kamata ya zo wuri na, ya gaya mun wai yana son yin takaran wannan matsayin ba.

107. **TANKO:** **(SLY)** Ko don Hassan na tunanin cewa ba sai ya zo bane domin ba kowa ke girmama matsayinka na me na*d*a sarakai a wannan garin ba.

108. **ALHAJI:** Kalli Tanko, ina ganin cewa akwai rashin fahimta a nan. Bayan duk taimako da nayi wa iyalinsa? Sai na san gaskiyar maganar!

109. <u>**BRIDGE MUSIC AND ENDCREDITS**</u>